# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na huɗu: Ɓatan kai a Turai

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Suleman: | ɗan shekara 19 |
| Mamman: | ɗan shekara 24 |
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Ma’aikaciya: | ’yar shekara 30 |
| Mace | |
| Namiji | |
| Mai shela: | ’yar shekara 35 |
| Jami’in tsaro: | ɗan shekara 40 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa a shirin namu na "Ji Ka Karu" wanda shi ne kashi na huɗu a jerin wasanmu na wannan gidan rediyo mai suna "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". A wancan shirin, Lami ta yi sallama da ƙasarsu ta kuma kama hanya zuwa Turai don ci gaba da karatunta. A cikin jirgi ta haɗu da wata mata mai suna Sa'adatu, kuma nan take suka zama ƙawayen juna. A can wani wuri kuma, Faisal mai shirin yin gudun hijira ta haramtacciyar hanya ya gamu da abokinsa a wani shagon intanet. Hakan kuwa ya faru ne jim kaɗan bayan ya rasa da motar masu safarar 'yan gudun hijira wadda da ya same ta ita ce za ta ɗauke su daga garinsu zuwa Turai ta ɓarauniyar hanya. To, ko me zai faru a wannan wasan na yau? Ku biyo mu, don kuwa mun kusa jin hakan. Wannan wasan namu na yau dai sunansa "Ɓatan kai a Turai".

Bari mu fara da su Faisal da Suleman a cikin shagon intanet. Shi dai Faisal yana hira ne da wani abokinsa mai suna Mamman wanda shi tuni ya riga ya shiga Turai inda kuma yake neman mafaka.

**Fitowa ta 1: Faisal da Suleman a shagon intanet**

**Suleman:** Haba Faisal! Wai da wa kake *skyping* ne tun tuni? Ina ta jiranka, yanzu na fi awa ɗaya.

**Faisal:** Ina zuwa don Allah Mamman, ɗan ba ni mintin ɗaya. … Mene ne ke damunka ne kai kuwa? Ba ka ganin abin da nake? Ka jira ni mana don Allah!

**Suleman:** Aikin ke nan da ma da nake ta yi. Shin ma da wa kake *skyping* ɗin ne? Iye? Yanzu haka ma yarinyarka ce!

**Faisal:** Kai, ba na son shirme! Wani abokina ne wanda shi ya riga ya sha. A halin yanzu ma yana neman mafaka a Turai. Yana ma ba ni labarin yadda rayuwarsa ta canja ne.

**Suleman:** Rayuwarsa ta canja? Kamar yaya, ta waru ko abubuwa sun rikice?

**Faisal:** Ta waru dai! Ka ga, ɗan jira ni kaɗan, ba zan daɗe ba. Ka ga ina asarar *airtime* ɗina garin magana da kai! Je ka mana! … *Sorry* Mamman don Allah! Kana ba ni labarin cewa askarawan bakin teku suka gan ka sai suka raka ka cikin gari. To sai aka yi yaya?

**Mamman:** Wallahi, sai suka ba mu barguna da abinci, sannan likita ya dudduba mu. Wasu daga cikinmu ma kusan duk ruwan jikinsu ya ƙare, wasu kuma ba su da cikakkiyar lafiya.

**Faisal:** Wato dai an kula da ku sosai!

**Mamman:** E to… haka ɗin ne. Ka san Turai ce, haka tsarinsu yake.

**Faisal:** Ko ka san lokacin da kwale-kwalen zai dawo?

**Mamman:** Kai! A'a, amma da zarar na ji lokacin zan yi maka *text* in sha Allah. Bari in yi sauri don in koma *hostel*.

**Faisal:** Kai *guy*, amma ina ma ni ne kai! To na gode, Mamman. Sai mun yi magana.

**Mamman:** To, na gode, Faisal.

**Mai ba da labari:**
Faisal dai yana sha'awar abokinsa da yake Turai yake kuma neman mafaka. To ko yaya rayuwar mai neman mafaka take kuwa? Ku dai biyo mu, za mu ji yadda abin yake nan gaba kaɗan. A ɗaya ɓangaren kuma, washegari da

sassafe Lami ta sauka lafiya a filin jirgin wata ƙasar Turai inda za ta shiga wani jirgin zuwa garin da makarantarsu take. Bari mu ji ko yaya za ta yi.

**Fitowa ta 2: Lami a wani filin jirgin sama a Turai**

| | |
|---|---|
| **Lami:** | Ni 'yan nan! Irin wannan filin jirgi haka makeke! Sai hada-hada ake ta yi! Saura minti arba'in kacal na shiga wani jirgin kuma. Yauwa, bari na tambayi wannan matar ko za ta faɗa min yadda zan yi. … Don Allah ji mana Madam, ina kwana? Ko kin san inda... |
| **Mace:** | Kin ga, saurara! Sauri nake zan shiga jirgi. |
| **Lami:** | To!? Wannan wane irin abu ne? Ba ta ma bari na ƙarasa tambayata ba! Mhm, bari na tuntuɓi wancan mutumin da yake zaune yana karanta jarida. … Sannu dai! Ina tambayar ta inda zan bi ne... |
| **Namiji:** | Ni ma ban sani ba. Ni ma yau na taɓa zuwa. |
| **Lami:** | Wannan wacce irin ƙasa ce! Kowa sai harkar gabansa yake yi kawai. Yauwa, Allah na gode maka! Ga mai bayar da bayanai can! … Sannu da aiki, don Allah ko za ki iya faɗa mini inda kofa ta biyar take? |
| **Ma'aikaciya:** | Ai 'yammata sai dai ki dinga bin alamomin nan, an rubuta komai ɓaro-ɓaro a kan alamomin. Ki miƙe, sai ki yi dama, ki fice daga cikin ginin nan, sai ki isa zuwa ɓangaren filin jirgi na biyu, sannan ki hau wani inji mai matattakala zuwa ginin masu jiran tashi. Daga nan za ki je inda za a caje ki, sai kuma ki wuce zuwa ƙofa ta biyar. Sauka lafiya. |

**Lami:** Wayyo Allahna! Kai, ni na manta ma abin da ta ce da ni. Inda za a caje ni? Kai! Ai kuwa lokaci ya kusa ƙurewa. Bari na yi sauri!

**Mai ba da labari:**
A ɗaya ɓangaren kuma a can arewacin Afirka, Faisal ya samo wata hanya mafi sauƙi da za ta taimaka musu shi da Suleman wajen shiga Turai. Ga shi nan yana ƙoƙarin faɗa wa Suleman yayin da suke tattaki a gaɓar teku.

**Fitowa ta 3: Faisal da Suleman a gaɓar teku**

**Faisal:** Kana ji ko Suleman, ina ganin me zai hana mu yi amfani da kwale-kwalen babanka mu haye teku. Ka ga idan muka yi haka, ba za mu ba wa 'yan fasa-ƙwaurin nan ko kwabo ba saboda sun cika tsauwalawa.

**Suleman:** Hahaha! Lallai ka zo da dabara. To ta yaya kake ganin hakan zai faru? Haba Faisal, ya kamata ka yi tunani!

**Faisal:** Wallahi da gaske nake yi! Ina ganin tun da kai ka gaje su, ya kamata a ce ka san wani abu game da kwale-kwale da kuma teku.

**Suleman:** Wai da gaske kake yi kuwa? Ni fa na ɗauka da wasa kake yi. Haba Faisal, na yadda babana masunci ne, amma sai me? Ba za mu iya zuwa Turai mu kaɗai a cikin wani jigari-jigarin kwale-kwale ba. Ba inda zai kai mu.

**Faisal:** 'Yan gudun hijira su biyu a ɗan karamin kwale-kwale sa iya samun nasarar shiga Turai fiye da 'yan gudun hijira ashirin ko ma hamsin a wani ƙaton kwale-kwale.

**Suleman:** Kai, ba zai yiwu ba! Ba ka tunanin…

**Faisal:** Ina yi mana Suleman! Ka ga Suleman, muna fa da damar da yawancin mutane ba su da ita. To, me zai hana mu yi amfani da ita?

**Suleman:** Mhmm… to, amma... amma... To, shi babana kuma yaya zai yi ke nan? Dukkan mutanen gidanmu masunta ne. Ba zan iya sace masa kwale-kwalensa haka nan ba, don kuwa da shi yake neman abinci. Zai iya tsine min na lalace!

**Faisal:** Wa ya ce sace shi za a yi? Hahaha. Kai! Ka je ka same shi ka faɗa masa abin da muke shirin yi. Na tabbata zai ba mu aron kwale-kwalen. Kowanne uba zai yi murna da jin ɗansa yana neman yadda zai yi don ya tsaya da ƙafafunsa. Idan kuma muka yi nasara, ’yan’uwanka sai sun fi morar abin.

**Suleman:** Kai! Duk wannan tunanin na tafiya Turai ya sa ka zama wani iri Faisal! Ka kuwa san halin babana? Sam! Ko kusa ba zan iya ba. In kuwa ka dage a kan wannan shirin, sai dai ka je ka same shi da kanka kai kaɗai.

**Faisal:** Kai Suleman! Wai yaushe za ka girma ne? Kusan kullum a idanunmu ɗaruruwan mutane ke wucewa ta garinmu zuwa Turai. In dai har wasu za su yi haka, to me zai hana mu ma mu yi? Na kuma gaya maka cewa ina da mutane a can, idan muka je, to ba abin zai dame mu.

**Suleman:** Gaskiya ne Faisal, wannan shirin kam ya yi. Amma me zai faru, misali idan kwale-kwalen namu ya kife fa? Ko kuma wani naman ruwan ya far mana? Ko kuma ma wata igiyar

ruwa ta yi wuji-wuji da mu, wanda hakan na iya sa mu sami kanmu a wata nahiyar maimakon Turai. Wannan ma fa abin da ka iya samunmu ne a hanya. Ga shi ba mu san me za mu tarar idan muka isa can ba.

**Faisal:** Ai ko'ina ta kwana sha ne, Turai ko Amurka! Muhimmin abin shi ne, mu bar wannan nahiyar tamu mai cike da talauci!

**Suleman:** Kai Faisal, sai ƙofofi kamar cali. Da ma siyasa ka shiga wallahi!

**Faisal:** Allah Ya kiyaye! Ai 'yan siyasarmu da shugabanninmu su ne suka jefa ƙasarmu a wannan mawuyacin halin. Ba abin da suka sani illa su wawashe dukiyar talakawa su cika aljihunsu. In kuwa suka ɗare kujerar mulki, sai sun bi duk wata hanya da za su tabbata a kan mulkin, ko da kuwa ta kowace irin hanya ce!

**Suleman:** E, gaskiya. Amma ka san, ban taɓa sanin kana da kishin ƙasarmu haka ba saboda kullum ba ka da wata maganar da ta wuce ta Turai.

**Faisal:** Ai dalilin shi ne saboda babu wani abin ku-zo-ku-gani da mutum zai ce a wannan ƙasar tamu. To, mu koma kan maganarmu. Yaya kake gani?

**Suleman:** Abin yana da haɗari ƙwarai, Faisal. Amma... ba komai. Ya kamata mu gwada mu gani.

**Faisal:** Yauwa! Amma ka burge ni! Yanzu ba abin da ya rage illa mu yi wa babanka magana. Ka san da zafi-zafi a kan bugi ƙarfe.

**Mai ba da labari:**
A can kuma filin jirgi, Lami tana ta faman neman ƙofar da za ta bi don ta ci gaba da tafiyarta, amma sai ga shi ta maƙale a wani dogon layin binciken jami'an tsaro. Kwatsam sai…

**Fitowa ta 4: Lami a wurin binciken jami'an tsaro a kan hanyarta zuwa garin da makarantarsu take**

**Mai shela:** Ina Lami Talle? Ki hanzarta ki ƙaraso ƙofar ta biyar. Kin tsayar da mutane. Kowa ya shiga jirgi, ke kaɗai ake jira.

**Lami:** Ni ake nema! Ni ake kira! Don Allah ku yi haƙuri na shiga gaba! Ku yi haƙuri, na wuce don Allah, jirginmu yana shirin tashi! Don Allah Malam, ku yi haƙuri, sauri nake ji!

**Jami'in tsaro:** Cire belt ɗinki da agogonki da duk wani abin da yake da ƙarfe daga jikinki. Mu ga *passport* ɗinki.

**Lami:** Ji mana Ofisa, don Allah ka ƙyale ni kada a tafi a bar ni. Yanzun nan suka kira sunana ta lasifika.

**Jami'in tsaro:** Akwai *laptop*, ko wani abu mai ruwa-ruwa ko wani abu mai kaifi a jakarki ta hannu?

**Lami:** A'a! Don Allah ni fa sauri nake kada a tafi a bar ni!

**Jami'in tsaro:** Kin ga 'yammata, daina ɗaga murya. Bi ta cikin waccan na'urar.

**Lami:** To, na gode.

**Mai gabatarwa:**

Ayya! Shigar Lami ta cikin na'urar ya sa injin ya yi ƙara! Shin za ta isa ga jirgin kafin su tashi kuwa? Sai ku biyo mu zuwa kashi na gaba don jin yadda za ta kasance a cikin wannan wasan kwaikwayon namu mai suna “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan gudun hijirar 'yan Afirka zuwa Turai”. Waɗanne matsaloli Lami za ta ci karo da su a kan hanyarta ta zuwa jami'ar da za ta yi karatu a Turai? Shin Faisal da Suleman za su iya shawo kan baban Suleman ya ara musu kwale-kwalen nasa kuwa? Waɗannan da ma wasu bayanan za su zo a cikin kashi na biyar. Saura da me, ku biyo mu a adireshinmu na facebook.com/dw.lbe don ku tattauna a kan yadda 'yan gudun hijira, daga Afirka zuwa Turai a karo na farko kan samu kansu da yadda tunaninsu yake a kan Turai. Sai mun sake saduwa. Ku huta lafiya.